Ba'a taɓa ba wa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - zabi ba tsakanin abubuwa biyu face sai ya zaɓi mafi sauƙinsu, matuƙar bai kasance saɓo ba, idan ya kasance saɓo ne to ya kasance ya fi kowa nisantar shi

Daga Nana Aisha Uwar Muminai - Allah Ya yarda da ita - cewa ita ta ce: Ba'a taɓa ba wa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - zabi ba tsakanin abubuwa biyu face sai ya zaɓi mafi sauƙinsu, matuƙar bai kasance saɓo ba, idan ya kasance saɓo ne to ya kasance ya fi kowa nisantar shi, kuma Annabi bai bai taɓa ramuwar gayya ga kansa ba ko sau ɗaya, sai dai idan an keta hurumin Allah, sai ya yi hukunci saboda Allah da ita.

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Uwar muminai Nana A'isha - Allah Ya yarda da ita - ta bada labari game da wasu daga ɗabi'un Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -, daga abinda ta ambata: Cewa shi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ba'a taɓa ba shi zaɓi ba tsakanin al'amura biyu sai ya ɗauki mafi sauƙinsu muddin dai mafi sauƙin ba mai kaiwa zuwa zunubi ba ne, to cewa shi zai kasance mafi nisantar mutane ga wannan zunubin kuma zai zaɓi mafi tsanani a lokacin. Kuma (Annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi bai taɓa ramuwa ba ga kansa a keɓance ba, kai ya kasance yana kau da kai kuma yana afuwa daga haƙƙinsa sai dai idan keta alfarmomin Allah aka yi sai ya zama ya yi hukunci saboda Allah, kuma ya kasance mafi tsananin mutane a fushi saboda Allah.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/6389